[27/08 à 11:07] MRS SADAUKI 💫: *MACIJIN CIKI...*🪱

```gajren labari```🪱

MRS SADAUKI 💫✍️

SADAUKARWA ga S REZA

FCWA ☀️

*Jan hankali*
*Macizai da ake samu a gidaje ana kashe su ne bayan an kira su sau uku su fita, saboda tsoron kar da su kasance cikin Aljanu, sai dai (nau'i biyu): Al-abtar da dhut-Tafifatan waɗanda ake kashe su koda a gidaje ne saboda Annabi (SAW)kawai ya haramta shi ga sauran macizai. _Al-Bukhari, babin farkon halitta n°3297 da n°3298 da Muslim, babin aminci, n°2233._ *- Al-abtar (الأبتر) shine wanda wutsiyarsa tayi gajere,* *- dhut-tafifatayn (ذو الطفيتين) shine wanda yayi ke zane biyu a bayansa.*
Wajibi ne a kashe waɗannan macizai guda biyu a kowane hali, saɓanin sauran da ake kashewa sai bayan an kira su su fita har sau uku, ta hanyar cewa misali: "Na kira ku ku fita daga gidana" ko kuma wani hukunci da zai yi gargaɗi ne kuma ya na nuna masa cewa an hana shi zama a gidan.

In duk mutum ya yi haka amma macijin bai fita ba,hakan na nufin ba aljani ba ne,in ma shi ɗin ne to bai cancanci darantawa ba a kashe shi.
Amma idan maciji ya kai masa hari, sai a bar shi ya ture shi, ko da a karon farko. Idan har hakan ya haifar da kashe maciji ko kuma a iya dakile harin ta hanyar kashe shi, to a nan muna da hakkin yin hakan, kare kai ne. _Fatâwa Islamiyya juzu'i na 4, shafi na 450 da 451._ _Sheikh Muhammad Ibn Salih Al-Utheymine(r)_

*Page 1*

MACIJI ne! Tabbas idona ba gizau ba ne suke mini,jinjirin maciji ne a gabana.Kashin da nake mugun ji ne ya ɓace ɓat,sai murɗawa ciki hadi da ƙugi kamar mai jin yunwa."Sulululu"ya fara nufo inda nake,idonsa ƙurrr kaina ya na kallona,da sauri na rumtse nawa gam hadi da buɗe dukkan muryata na ƙwala uban ihu tare da neman agaji duk da na san gidan ni ɗaya ce Inna ta tafi kasuwa,Baba kuma ya na can gona tun safe.
```

Cikin tsoron da ya aure ni nake jiran farmaki haɗi da cizon MACIJIN sai dai ko ɗaya daga ciki.A hankali na buɗe idona da ke shatatar da hawaye,wayam babu macijin.Tamkar wacce ta yi ma sarki ƙarya haka na ci gaba da gwale ido ina duba ko ina na cikin banɗakin wanda ya kasance na kara.

Ina shafar ido na ɗauki butar da ta saɓile a hannuna tun lokacin da mu ka yi gamdakatar da maciji.
Waje na fito na ajiye butar tsakar gida,na shiga ɗaki.Ga mamakina Inna na tarar zaune kan tabarma ta na ƙirga kuɗi.Na ɗan turo baki gaba bisanin nace "saboda Allah Inna ki na ji na ashe duk ihun nan da nake na neman agaji ke ta ƙirgon kuɗi ki ke? Wai yaushe ma ki ka dawo?"

Ba tare da ta ɗago ta dube ni ba ta bani amsa "tunda Allah ya yi ki da shegen tsoron tsiya ba doli ki firgice ba,daga rana irin ta yau kar na sake gani ko ji kin shiga banɗaki da hantsi gatse-gatse muddin ba ni gida"
"Rummacen da na ci jiya ne ya burkuta mini ciki,to in ban zawaye shi ba Inna ya ki ke so na yi ? In tsaya ya kashe ni?" Na faɗa ina mai zama kusa da ita.
Sai a lokacin Inna ta ɗago kanta,mu ka haɗa ido da ita.Yanayin idonta da kallon ya so tuna mini wani abu amma ba ta bani damar yin tunani ba ta jefo mini tambaya "Tuwalle ba ki so mu yi kuɗi ne mu fita daga wannan ƙangin rayuwar?"
Ba tare da yin wani dogon nazari ba na bata amsa da "ina so mana Inna ,ni da nake son mu je can binni kullum mu rinƙa dafa macarandi da naman kaza"
"Yauwa Ramatuwalle na! To muddin ki na son mu je binni doli ki rinƙa yin duk abin da nace ki bar kuma wanda ban so"
"To Inna daga yau zan rinƙa yi" na faɗa ina susar daƙwalon kaina wanda yake jibge da ƴar karen dauɗa kamar mai jegon ƙauye.

"Saura ƙiris ya rage kuɗin da za mu fara sana'a su cika,da zarar sun kammala zan sayo kayan miya sai mu na kasawa a kasuwa" Inna ta faɗa ta na ƙulle kuɗin cikin baƙar leda bayan ta ware ɗari biyu.
"Inna mi za mu ci yau?" Na tambaye ta.
"Oh! Ni Tuwalle kin cika gaggawa kamar zawo! Ungo je ki gidan Mairo ki sayo mana kafa sai mu kwaɗa dama ina da sauran ƙuli"
Na waro ido haɗi da dafe ƙirji nace "Inna wannan matar fa mayya ce!"
Inna ta ce "wa ya faɗa miki mayya ce?"
Cikin son ƙin zuwa aiken na kwaɓe fuska na ce "Allah Inna mayya ce,duk ƙauyen nan babu wanda bai san Mairo na da *MACIJIN CIKI* mai tsotse jinin mutane shi ya sa ba kowa ke shiga gidanta ba"

Ga mamakina sai na ga Inna ta haɗe rai ta gimtse fuska kicin-kicin kai kace Mairo ɗin uwarta ce.
"Daga yau kar na sake jin kin faɗi haka,abin da mutane ke cewa ba doli ya zamana gaskiya ba.Tashi maza ki karɓo mini "
Jiki a saɓule na miƙe tare da karɓar kuɗin na fita.
Babu wani nisa sosai tsakanin mu da gidanta.Kamar kullum gidan a rufe yake sai da na bubuga ,ina nan tsaye kamar kayan shanya don na fi minti biyar a tsaye sai faman kishin gidan nake. Har zan juya na ji muryarta "tsaya Tuwalle gani nan!"
Na harari ƙyauren gidan ina gunguni,ta buɗe ta na mai tambayata"Asabe ta aiko ki?" Ta na nufin Innata,kai na ɗaga mata tare da miƙa mata kuɗin nace "kafa za a bani" "ki shigo mana "ta faɗa ni kuwa na yi tsaye ƙiƙam na riƙe ƙyaure a zuci nace ' na shigo ki tsotse mini jini ko?'
"Ki shigo ki karɓa" ta ƙara faɗa a karo na biyu ta na mai juyowa ,zuciyata na bugun uku-uku cike da tsoro na shiga amma a tsakar gida na tsaya .

Ina nan tsaye ina jiran ta fito sai ji na yi mage na shafar mini ƙafa.Na yi tsalle na ja da baya,amma abu kamar na tsiya magen nan ta saka yatsunta ta karce ni a ƙafa.
Na yi ƙara haɗi da rugawa na shige ɗaki,tamkar munafuka haka na yi tsaye cikin ɗakin ina rarraba ido.
Abun da ya bani mamaki shi ne yadda Mairo ta buɗe labulen ɗaki ta shigo,alhalin dama tun can ta na cikin ɗaki.
'To yaushe ta fita ? ' ban sani ba.

Fuska a haɗe ta ɗauki leda ta zuba mini kafar,ta miƙo mini tare da mini wani kallon irin kamar ya ki ka gani? Gobe ma ki sake.Amma da yake ni ɗu ce ban fahimci komi ba haka na karɓa,na zo na kawo ma Inna .

Da dare ina bacci,ƙafata ta ishe ni da zugi.A doli na tashi zaune,na fara sosa gun.Jin tamkar ana ƙara mini zafin ya saka ni fashe wa da kuka.
Baba da ke can ƙurya ɗaki shi ya fito ya na mai hasko ni da fitila "lafiya mine ne?" Ya tambaye ni,ƙafar na nuna masa da sauri ya zauna ya na mai tambayata "mine ne ya ji miki?"
Shiru na yi don har ga Allah na manta magen Mairo ta yage ni.
"Bari sosa wa kar ya yi jini" ya faɗa tare da fara tofa mini addu'a.Cikin ikon Allah na ji komi ya tsaya,hakan ya sa na raɓa gefen Inna wacce ke ta yin bacci kamar matatta.
A gaban idona Baba ya haskata da fitilar hannunsa,duk da akwai hasken ƙwan fitila aci balbal.Kai ya girgiza ya ce "Allah shirya!" Ban san mi ya gani ba ko mi yake nufi da hakan ba kawai dai na lumshe idona.

Kwaramniya ko nace haniyar su ce ta tashe ni daga bacci.
Ban san mine ne ya haɗa su ba,haka ban san farkon rikicin ba kawai tashi na yi na ji su na faɗa da junansu.
Na buɗe na zomayena na fara sauraren masayar yawunsu.
Inna ce ta ke faɗar "babu ruwan ka da rayuwata,ka yi taka in yi tawa.Ina ce dai abincin da za mu ci ka na baƙin cikin kawo wa,ni ce dai wacce ka ke kira da mayya,bokanya nake fita nake nemowa"

Baba ya katse ta "ki ke nemowa ko ki ke satowa? To bari ki ji wlh daga yau in na sake ganin mugayen halayen ki sai kin bar gidan nan"
"Ai wlh sai dai kai ka bar shi amma ni zama daram"
"Asabe ki ji tsoron Allah,ki kasance uwa ta gari wacce ƴarta za ta yi koyi da ke"
"Na ƙi na zama,wai Audu da ka ke kuri ka ke tunƙawo kafin ka zama malami ina ce kai ne Sarkin may...."
Tarin da na yi ne ya saka Inna yin shiru,sai duk suka juyo suka zuba mini ido kamar masu son sanin tun yaushe na tashi.Fahimtar haka ya saka na fara murza ido,kamar wata ƙaramar yarinya na fara kukan sangarta tare da tashi ta na nufi ƙofa.
"Kar ki buɗe ɗaki safiya ba ta yi ba" cewar Baba.
"Ruwa zan sha" na faɗa a shagwaɓe,Inna ta harare ni ta mai cewa "su kuma ruwan da ke cikin moɗar ƙarfe"
Na sosa ƙeya tare da zuwa na ɗauki moɗar ƙarfen wacce dama kullum a cike take da ruwa saboda ko da mutum ya ji ƙishi.

Baba ya koma can ƙurya ɗaki,ni kuwa ina gama shan ruwan na kwanta.
Tsawon lokaci da kwanciyata sai na ga Inna na leƙon fuskata,da sauri na lumshe ido kamar mai yin bacci.
"Tuwalle? Tuwalle? Tuwalle?" Ta kira sunana har sau uku amma na yi shiru kamar ba na jin ta.

Ƙarar buɗe ɗaki na ji wanda ta yi shi a hankali,ban san ina ne Inna za ta je ba kawai dai na samu kaina da bugawar zuciya da sauri da sauri.
An ɗauki kamar minti goma da fitar Inna ,sannan na tashi zaune.Sauraren zuciyata nake wacce ke ce mini na fita na ga mine ne Inna ke yi,sai dai kiciniya da hargowar da kunnuwa suka fara jiyo daga waje ya katse mini hanzari.

Da sauri na sake komawa na kwanta,tamkar ana taron biki haka nake jin tsiminiyar mutane.Ina nan kwance ina tunani ban san lokacin da bacci ya ɗauke ni ba.

Washegari
Ina farkawa na fita,idona ba su gama buɗe wa taram ba na nufi banɗaki ko buta ban ɗauka ba.

Kamar jira yake na tsugunna,MACIJIN da na gani jiya ya sake ɓullo wa ta cikin zana......
[27/08 à 11:08] MRS SADAUKI 💫: *MACIJIN CIKI..*🪱

```gajren labari```🪱

MRS SADAUKI 💫✍️

SADAUKARWA ga S REZA

FCWA ☀️

*Page 2*

MACIJIN ya ƙure ni da tsanwayen/kori idonsa kamar dai jiya.Daga inda nake tsugunne fitsri sai ratata yake mini kai kace raƙumin da ya shanye ƙoramar ruwa.
Tamkar wacce aka shuka,na kasa tashi a gaban idona ya yi sulululu ya wuce.Tsawon kamar minti biyar na miƙe,ashe fitsari da zawo ne na yi ba tare da ni kaina na sani ba.
Ina kuka na fita daga ɗan kewayen zanan da ya kasance banɗaki,ruwa na samo na wanke jikina.
Ina shiga ɗaki na tarar da Inna kwance ta rufa da bargo ta na maida numfashi kamar dokin da ya gama tsere.

Jikinta na faɗa jikinta ,ina kuka da sauri kuma na janye tare da ƙoƙarin yaye bargon da ta rufa sai ta riƙe shi gam ta na mai juyo da fuskarta amma ba ta buɗe idonta ba.
"Inna? Inna mi ya same ki? Ina ƙafafun ki?" Na yi tambayar ina laluba can ƙasan ƙugunta sai dai wayam ba alamun ko ƙafa sai wani abu mai taushi da na ji gudan ƙatoto.

Cikin wata irin murya wacce ban santa da ita ba ta ce "je ki dubo Baban ki"
Ambaton sunan Baba ya saka na maida dubana da ƙofar shiga ƙurya ɗaki,ƙunnai haɗi da alamun jan ajiyar zuciya kunnuwana suka jiye mini.
Da sauri na shiga,cikin mawuyacin halin na tarar da Babana.Ban san lokacin da na fara yin kuka ba ina kiran "Baba? Baba?" Tuni idonsa sun kafe,sai bakinsa da yake motsawa kafin wani lokaci tsit babu gurnani babu numfashi.

Daga bayana na ji Inna na tambayata "ya jikin nasa?"
Na juyo ido shaɓe-shaɓe da hawaye na ce "Inna tun yaushe Baba ya fara rashin lafiya ba tare
```

da na sani ba?"
Ba ta bani amsa ba kawai sai gani na yi ta matsa kusa da Baba,idonsa ta shafa tare da lulube shi har izuwa kai sannan ta ja hannuna mu ka fita.

"Allah ya yi ma Baban ki rasuwa!" Shi ne abin da Inna ta faɗa mini,ko kaɗan ban ga alamar rauni ko ƙunci a tattare da matar da ta rasa mijinta sai ma wani farin ciki.
Tamkar saukar guduma haka na ji,ihu da kururuwar da nake shi ya jawo hankalin maƙwabta.
Kafin wani lokaci mutanen ƙauyenmu sun hallarci zana'izar Babana.
Tamkar sabuwar amarya haka ƙawayen Inna suka kewaye ta su na ta shan hirar su,ban san mi su ke cewa ba amma ban ga alhini a fuskokinsu ba.

"Kai Asabe mijin nan naki ya cika taurin rai,yaƙi kamar ba gobe! "

"Ki bari ni har sai da na sare na zata ba za mu iya kai shi ƙasa ba"

"Yanzu dai ke ma kin huta da alaƙaƙai!"

"Ba ki ji sanyi a ranka ki ba da ya zamana babu wani wanda ya san sirrin ki?"

Abokan Asabe ne ke tattaunawa game da yaƙin kashe mijinta da suka taya ta a jiya wajen kashe mijinta Audu.Shiru ta yi ta na saurarensu,rabin hankalinta ya na kan Tuwalle wacce ke can zaune a rakuɓe ɗan nesa da su.Fahimtar haka ne ya saka Mairo cewa "wai mine ne? Ko ita ma Tuwallen ki na so ta bi Babanta ne?"
Da sauri Asabe ta dubeta,ta wani taɓe baki "hum! Duk wannan abin da naka don waye nake yi? Saboda Tuwallen ne! Saboda ina son gobenta ta yi kyau."
Mairo ta ce "ai na ga kamar kin damu ne sosai sai kallonta ki ke"
"Eh ina tausayinta ne,na san za a ɗauki lokaci kafin mutuwar ta fita ranta"
"Wannan ai ba damuwa ba ne,akwai wani magani da nake da zarar ta sha shi to shikenan za ta sakin ranta ta ci gaba da walwala " ɗaya daga cikin matan mai suna Bintoto ta faɗa.

"Mutanen ƙauyen nan sam ba su da kara dubi duk sun watse ko awa ɗaya ba ayi da kaudo gawa ba " cewar Salame,Bintoto ta karɓe da cewa "saboda sun ga Mairo ne ,kin san kusan duk tsoronta ake a ƙauyen nan"

Cikin jin haushi Mairo ta ce "ina ce dai ba ni ɗaya ba ce mayya ,duk ɗaya nake da ku"
Duk suka yi dariya, Bintoto ta ce "to ai taki ce ta fito a fili,sam ba ki iya takun saƙa ba"

"Ku yi shiru" cewar Asabe.

Na gaji da zama cikin rana,hakan ya sa na tashi tare da nufo inda suke.A gaban idona Inna ta yi masu alama da hannu,duk da banda tabbaci amma na fi tunanin kamar ba ta so na ji hirar da suke.

Ban wani tsaya ɓata lokaci ba,ina zuwa na zauna kan tabarma tare da yin kwanciya na ɗora kaina bisa cinyar Inna.
"Ƙatuwa da ke shi ne ki ka wani zo ki ka yi kwance kan ƙafafuwanta" cewar Salame cikin sigar wasa ta yi maganar ta na ƴar dariya.
"Duka nawa take? Shekaru sha uku ɗin,kar ku takura ma auta ta" Inna ta faɗa ta na ɗan bubuga bayana.

"To ku tashi mu tafi sai in mun haɗe zuwa dare ko?" Mairo ta faɗa ta na mai tashi tsaye, Allah na gani sam na tsani matar nan.
Duk sauran tashi suka yi su ma,hira suke a jirkice wacce sam ban kanta ba balle ƙafafu.

Su na fita,sauran matan ƙauyenmu suka fara shigowa su na yi ma Inna ta'aziya.
Haka dai aka yi ta shigowa na tsawon kwana uku bisanin ƙafa ta tsana.

Hum! Ban san a ina Inna ta samu kuɗi ba kawai dai na ga ta yo sayayyar kayan miya.Irin su magi,garin kwaki,gishiri,tafarnuwa da dai sauran su.

Bayan ta gama ƙulle kayan miyar cikin leda sai ta zuba cikin faranti.
"Zo ki shiga gidaje ,ko Allah yasa kin yi cinaki." Inna ta faɗa ta na kallona,na turo baki ina jin haushin yadda Inna sam ba ta damu da mutuwar Baba ba.

"Zo na aike ki gidan Salame ,ki ce mata maganin da tace za ta bani na aiko ki amsa" Inna ta faɗa cike da kulawa,na miƙe tsaye tare da kakaɓe burgujejen bujena.
Har zan tafi sai kuma Inna ta tsayar da ni "ungo ki kai mata daudawa da gishiri ,ki ce na fara sayar da kayan miya" na karɓa kafin na fita.

Ina tafe ina waƙa har na kai gidan Salame,sallama na ta yi ba a amsa ba.
Daga can cikin banɗaki ta ce "ina wanka ne ki jira ni" kan wani gutun ƙunƙu na je na zauna ina rera waƙa tare da wasa da kare ina yin zane.
Kamar daga sama na ga ƙatuwar tsutsa ta na fitowa daga wani ɗan rame alamu gidanta ne.
Yadda take shiga ta na fitowa ya ɗauki hankalina,ta saka kanta domin komawa cikin ramen kawai sai na saka karen da nake wasa da shi na cake bindinta tare da danne shi.
Ta ji zafi ne ko kuwa mine ne oho! Kawai dai na ga ta fitar da kanta daga cikin ramen tare da

kiciniyar janye bindinta.Cike da mugunta na hude ledar gishiri na fara zuba mata a jiki,na sani sarai tsutsa ba ta son shiga gishiri.
Yadda take birkiɗoɗoniya shi ya fi komi yi min daɗi,sai ƙara juyata nake ina zuba mata gishirin.
Sam ban jin tawowar Salame ba,sai saukar muryarta na ji "mine ne ki ke haka?" Da sauri na jefar da karen ina cewa "Ina kwana Inna Salame ? Inna ce ta aiko ni "
Ba ta amsa gaisuwar da na yi mata ba, sai kallon ƙasa da take yi ni ma na kai idona nan na yi tozali tsutsar nan a kwance kamar dai ta mutu.
"Da ta aiko ki sai ta ce ki zo ki yi mugunta?" Ta tambaye ni cikin zafin rai.
Sarai na fahimci abin da take nufi,amma ni ban ga wani aibu ba a nan don na cutar da tsutsa tunda ba Ɗan cikinta ba ne.

Ta ja tsuki ta shiga ɗaki,ba ta jima ba ta fito hannunta riƙe da leda.Ta miƙa mini na karɓa,sai nace "ga kayan miy..." Cikin haushi ta katse ni"na ji don Allah! Wuce ki tafi"

Yadda ta wakice ni sam ban ji daɗi ba, wannan ya saka na fita a guje.
Inda na yi sakarci da na zo gida maimakon na baiwa Inna labarin komi sai na yi shiru da bakina ashe babban kuskure ne.

Dare ya yi amma sam na kasa rumtsa wa saboda raɗaɗi da azabar da duk jikina ke yi mini.
Kuka kawai nake ina susar ko ina,bisanin na tashe da Inna .
Fitila ta haska mini,sai na ji ta na salati tare da ambaton sunan Salame....
[27/08 à 11:09] MRS SADAUKI 💫: *MACIJIN CIKI..*🪱

```gajren labari```🪱

MRS SADAUKI 💫✍️

SADAUKARWA ga S REZA

FCWA ☀️

*Page 3*

Cikin wannan tsohon daren Inna ta fita,ba zan ce kai tsaye gidan Salame ta nufa ba amma ina kyautata zato.
Ta ɗauki sama da minti talatin kafin ta dawo,wata tsohuwar ƙwarya wacce ban san daga ina ta
```

samo ta ba na ga ta ajiye a gabana bisanin ta fara yi mini wanka da ruwan da ke ciki.
A duk lokacin da sanyin ruwan ya ratsa fatata sai na ji duk raɗaɗin na fita a sannu-sannu,ban san iya minti nawa Inna ta yi ta na yi mini magani ba.Kawai na tsinci kaina cikin wani dadaɗan bacci .
Washegari ko da na tashi duk ƙaiƙayin ya fita haka ma birdin.Ban wani damu da na yi ma Inna tambayar ya aka yi hakan ta faru ba na ci gaba da harakokina.

Zuwa ƙarfe goma na safe mu ka je kasuwa ni da Inna.
Abu guda yake bani mamaki yadda duk a ƙi sayen kayan miyan kowa sai na Inna .Har gosulo aka yi wajen jira,farin cikin Inna kuwa ba a misalta shi.
Dandanan komi ya ƙare mu ka dawo gida.
"In sha Allah na kusa cika miki burin ki na zuwa birni, lokaci kaɗan ya rage"Inna ke faɗa ta na ƙirga kuɗi.
Na washe baki cike da murna na ce "Inna har da mota za ki saya mini ,da ƙaton gida ki zuba mini ƴan aiki wanda za su rinƙa yi mini hidima"

Inna ta tsaya kallona murmushi kan fuskarta ta ce "in dai ina raye Tuwalle ba za ki taɓa wahala ba"
"Yunwa nake ji Inna ,amma dai yau za ki dafa mana taliyar leda?"
"Ƙwarai kuwa! Har da ma ƙashi zan saka amma sai zuwa marice.Yanzu za mu yi kwaɗin garin kwaki"
Na kwaɓe fuska jin ta ambaci garin kwaki,Inna ta ce "har da fa digadigi zan saka miki,ko kuwa kin fi son niƙaƙar gyaɗa ?"
"Inna ni taliyar leda nake so" na faɗa ina hawaye.
"To mine ne na kuka? Ina ce dai kuɗin don ke nake neman su.Ungo ki je ki sayo,in sha Allah zuwa gaba ni ma har da taliyar ledar zan rinƙa siyar wa"

Kuɗin na karɓa ina cewa "na sayo har da ƙashin?"
"A'a ki bari sai na sayo mana balangu" ina gama sauraren amsar Inna na fice da gudu.
Bayan na sayo taliyar na dawo gida,turus na yi a bakin ƙofa ina kallon ikon Allah.

Mairo ce da Bintoto sun saka Salame a tsakiya sai suratai suke kamar uwanda suka hau bori yayin da Inna ta koma gefe ta na ƙullin kayan miya kai kace ba ta san da zamansu ba.
A hankali na tako har izuwa gun da Inna take , Bintoto ta yo kaina da sauri ta na cewa "Yauwa Tuwalle ki roƙi Innar ki ta saki Salame ba don halinta ba sai don zamen tare"
Ban fahimci abin da take nufi ba hakan ya sa na dubi Inna ,wacce ta tsaya da abin da take ta na kallona.
Kamar ba za ta yi magana ba sai kuma ta ce "ai a tunani ko bayan raina ko wani Salame ta gani zai cutar da Tuwalle za ta hana shi balle ita.Hum! Don Allah kar ku yi ɓarnar bakin ku ba zan yafe ba,ai duk tsuntsun da ya ja ruwa shi ruwa yake duka!" Inna na gama faɗar haka ta karɓi

taliyar hannuna ta je ta hura huta.

Mairo ta ce "Asabe tun ɗazu mu ke tambayar ki laifin da ta yi miki amma kin yi shiru"
Inna ta juyo ta bata amsa "ga kai ga fata,ai bai kai ku tambayi mi aka yanka ba.Ku tambayeta ta baku amsa"
Bintoto ta karɓe zancen da "wlh tun da safe muke ta faman tambayarta amma ta ƙi faɗa mana,yanzu ma da ki ga  mun zo nan dan mun san ke ki ke da MACIJI "

Ƙarshen furucin Bintoto na ambaton sunan MACIJI ya saka ni lulawa duniyar tunani wacce daga nan ban sake sani abin da suka tattauna a kai ba.
'kenan wannan MACIJIN Inna ne? To dama ana kiyon MACIJI ne? To a ina yake rayuwa? Inna ta ɓoye shi ne ' Ni ɗaya ke maganar zuci,Inna ta katse mini shi ta hanyar dafa ni tare da tambayata "Tuwallena ya ki ka gani a bar goggon Salame haka ko ya ya?" Duk da ban ida fahimtar tambayar ba,amma tunanina ya bani cewa amsar da zan bayar ita ce abin da Inna za ta ɗauka.
Kai na ɗaga mata ina kallonta.Inna ta ja baki ta ce "hum! Yaro da saurin mantuwa,jiya Salamen ce ta hana ta bacci yanzu kuma ana yi mata ramuwa amma har ta yafe" ta faɗi haka ne tare da shiga cikin ɗaki.

Ba ta jima ba ta fito da wata jaka irin ta fata,inda Salame take a kwance ta je ta zauna sannan ta fiddo wata ƴar gyanɗama.
Ban san ko mine ne a ciki ba,kawai dai na ga Inna ta taɓe bakin Salame ta zuba mata abin da ke ciki a baki.

Shure-shure ta fara bisanin ta zabura ta tashi zaune ta fara yin aman jini baƙi ƙirin.
"Alhamdullah ! Ta amayar da gubar" shi ne abin da Mairo ta ce.

Salame ta maida numfashi ta yi zaune ta na kalle-kalle har mu ka ido huɗu da ita.Wani mugun kallo ta yi mini mai cike da tsantsar ƙiyayya.Inna da ke gefenta ta tashi cikin ɗaga murya ta ce "jiki magayi! A kiyaye gaba,akan Tuwalle zan iya yin komi"

"Yanzu dai komi ya wuce"cewar Bintoto bisanin kuma ta ƙara da cewa "to mu zamu tafi sai zuwa dare in mun haɗu"
A kunyace Salame ta tashi ta bi abokanta.Su na fita ta ce "na tsani Tuwalle,jiya fa dodon tsafina ta zuba ma gishiri.Duk yadda na so na in jurewa kasawa na yi,shi yasa na ɗanɗana mata azaba amma sam ban yi tunanin Asabe za ta yi mini haka ba"
"Hum! Ke ma in ba abun ki ba,wa zai taɓa Ɗan BOKANYA (MRS SADAUKI,duk mai son littafin BOKANYA complete 500₦ zai iya mini magana +22795045822  ) a zauna lafiya? " Bintoto ta faɗa ta na gyara mayafinta.
"Tun da ƴar iskar yarinya ce mi zai hana kuwa? Ai ko ni wlh haushi take ban  " cewar Mairo.

"Za mu yi maganinta ne" Salame ta faɗa.
Bintoto ta ce "Ni dai babu ruwana kun san halin Asabe ba ta da daɗi "
A haka suka ci gaba da tafiya har suka kawo hanyar da za su rabu da juna kowa ya nufi gidansa.

Su na fita na ce "Inna dama wannan MACIJIN na gidanmu ne?" Banza ta yi da ni,na zata ba ta ji ba ne hakan yasa na sake maimaita tambayar .Kallona kawai ta yi ba ta ce komi ba,na turo baki gaba na ce "Inna tambayar ki fa nake"
"Yi mini shiru dallah,sai shegen surutun tsiya.In na sake jin kin yi zancen MACIJI ni da ke ne"Inna ta wakice ni haɗi da yi mini faɗa.
Haushi na ji sosai kawai sai na fashe da kuka.Sam ba ta kula ni ba,sai ma girkinta da take.Har ɗaga murya nake ina birkiɗa da ƙasa don ta ban haƙuri kamar yadda ta saba tattalina amma Inna ta yi biris da ni.
Wannan ya saka ni kuma da ta gama girkin na ƙi cin abincin.
"Hum! Tuwalle rayuwar ki sai ke! Yanzu abincin ma sai kin yi fushi da shi? Zo yi haƙuri ki ci" Inna ta faɗa ta na kamo hannuna,abun ka ga Ɗa da mahaifi sai na miƙe na bi bayanta.
Sai da ta cika buta da ruwa ta mini wanka sannan ta zaunar da ni kan tabarma ,abinci ta zuba mini cike da kwano na yi masa tas na suɗe kwano na sha ruwa na kwanta ina lumshe ido.

Sai wuraren magrib na farka,da na tashi ban ga Inna ba.Na duba ɗaki ba ta nan,har zan fita ƙofar gida sai na tsinkayeta can bayan kewayen zanar banɗaki.

Ban san mine ne take ba saboda ta bani baya,a hankali na taka har zuwa gunta.
"Inna...." A zabure ta juyo ba tare da ta bari na ida maganata ba sai kuma ta yi saurin maida ƙasa ta rufe wani rame wanda ban san miye a ciki ba.
"Tuwallena kin tashi?" Ta tambaye ta na mai miƙewa tsaye,na gyaɗa kai ina mai duben inda ta zuba ƙasa nace "Inna mine ne ki ke?"
Ba ta bani amsar tambayata ba ta ja hannuna mu ka koma can ƙofar ɗaki.

"Na zuba miki fura ? Ko ba ki jin yunwa?" Ta tambaye ni,Allah na gani ni ba wannan nake son ji ba,kawai abin da ta rufe da ƙasa nake son sani don Allah ya yi ni da wani hali bin ƙididdiga da shiga abin da bai shafe ni ba.

"Wanka zan yi" na faɗa ina hamma,Inna ta dube ni da kyau ban san mi ta gani cikin idona ba sai ce mini ta yi "Ramatuwalle mi yasa ba ki jin magana? Daga yau ina miki hani da bin

ƙididdiga da shishigi,ba komi ba ne na rufe gashin kaina ne da ya zuba lokacin da nake kwance kitsona"

Shiru na yi ,don kuwa Inna ta karanci abin da ke raina.Dama ba wankan ne a gabana ba kawai ina son zuwa na tone ramen da ta yi ne.
Na ɗan turo baki gaba jin ta halbo jirgina na ce "shi ne kuma tun ɗazu da na tambaye ki ba ki faɗa mini ba? Ni na yi tunanin ko MACIJIN ki da na ji su goggo Mairo na faɗa ne ki ka kashe tunda ya zama mugu har ya fara cizon mutane"

"Je ki share mini ɗaki" cewar Inna ,da saurina na tashi na ɗauki tsintsiya na yi shara.
Inna ta gyara mana shimfiɗa sannan ta kunna fitilar ƙwai wacce ake zuba ma petur.

Sai da na sake cika cikina ƙui-ƙui sannan na kwanta ina maida numfashi kamar tsohon  ciki.
Ina cikin bacci na ji warin wani abu a hancina,da sauri na sa tafin hannu na goge shi tare da gyara kwanci sai dai kamar wacce aka tsikara firgit na yi na ida tashi daga baccin.

Babu Inna kan shimfiɗa,na duba ƙofar ɗaki kuma sai na ga a rufe take.Fitila na ɗauka na shiga ƙurya ɗaki nan ma ba ta nan,har zan fito wani sauti ya ja hankalina da sauri na juya ina mai ƙara ɗaga fitilar hannuna ta yadda zan gani da kyau.
Cikin akwatin Baba ne ake motsi ,kamar wacce ake ɗingizawa haka na je na matsa kusa da shi na  f na saka hannuna guda na ɗaga marfin akwatin ƙara na ƙurma haɗi da sakin fitilar ƙwan.

A guje na yo falo jikina na mini rawa,ƙaton MACIJI na gani da wata baƙar mage sai ƙadangare.
Bisa shimfiɗata na haye tare da jan bargo na rufa ruf,sululu na ji wani abu mai sanyi ya na bin ƙafafuna wanda ya yi sanadiyar ɗaukewar numfashina.....
[27/08 à 11:10] MRS SADAUKI 💫: *MACIJIN CIKI..*🪱

```gajren labari```🪱

MRS SADAUKI 💫✍️

SADAUKARWA ga S REZA

FCWA ☀️
```

*Page 4*

*Ashe 4 ne zan saka sai na saka page 5 ku yi haƙuri ga shi nan na gyara*

Wani irin abu mai kama da hadarin sama ya rufe ni.Bugun zuciyata kuwa fat! Fat! Fat! Kawai yake fita tamkar wacce ta yi gudun fanfalaƙe.
A zuwa yanzu zan iya cewa MACIJI ne yake bi mini jiki sakamakon taushi da kuma jelarsa da nake jin ta na gugar fatar jikina.

Ta ƙarƙashin rigata ya fito,cikin kunnena na ji an ɗiga mini wasu ruwa masu yauƙi wanda nake kyautata zaton yawunsa ne.Ina jin yadda ruwan ke kwaranya can cikin mahudar kunnena,ha na ji wani abu ɗimmm .Numfashina ne ya fara canza yanayin tafiya,daga nan ban sake sanin abin da ya faru ba .

Inna macijiya ta ja wani dogon numfashi ganin ta sake mayar da Tuwalle cikin halin matsanancin bacci.
Sulululu ta fito daga cikin rigar Tuwalle ta koma ƙurya ɗaki cikin siffarta ta MACIJI .Cikin akwatin ta koma ta tarar da abokanta sun yi tsuru-tsuru ko wace ita ma siffar mugunta.
Mairo ita ce mage, Bintoto kuwa ƙadangaruwa.

"Ya haka Asabe? Ki ka ce sai da ki ka shafa mata mai a fuska wanda zai ƙara nitsata cikin bacci,yanzu kuma ta gan mu sai ya ya kenan?" Mairo ce ta yi tambayar ta na kallon Inna Asabe da wuƙi-wuƙin idonta .
" wlh sai da na shafa mata shi,yanzu dai ta koma bacci" cewar Inna Asabe.
"Hum! Duk cikinmu ke ɗaya ce ke Ƴa,tun tuni na so ki kawar da ita amma ki ka ƙi" Mairo ta sake faɗa.
Inna Asabe cikin fushi ta ce "kin ga Mairo ta ya zan kashe Ƴata? Sanin kan ki ne ni ba mayya ba ce balle ace na kasa haɗiye yawuna,tsafi kawai nake"
"Mu ki bamu in ba ki so"
"Eh lalle Mairo yau na tabbatar ba ki da hankali,wato Ƴar tawa zan baku ku cinye sai kace wata kaza? Yaran ku da ku ka ci ma rashin sanin ciwon kai ne"

Bintoto ce ta katse Inna Asabe ta na cewa "don Allah ku bar wannan zancen ku zo mu yi abin da ya haɗa mu a nan.Asabe ke ce ke da ƙarfin tsafi,ke za ki yi mana jagora zuwa gidan Mai Gari daga nan mu kuma sai mu san yadda za mu kashe shi"

"Taimako guda zan yi maku,shi ne zan saka duk al'ummar ƙauyen nan cikin dogon bacci ba za su tashi ba har sai kun kammala aikin ku." Cewar Inna Asabe ta na wani wasa da halshenta na MACIJI .

"Mu biyu ba za mu iya kashe Mai Gari ba,doli mu lalaɓo Salame ta biyo ayari.Sannan da ace sauran Mayun ƙauyen nan za su bamu hađin kai sai mu hađa ƙungiya" Mairo ta fađa da đan bakinta na mage.

"Ni dai babu ruwana can tsakanin ku ne,in ta na so ma daga yau ta ajiye kambun maita babu ruwan Asabe "
"Ya kamata mu tafi kar wuri ya ƙure mana" cewar Bintoto.
Inna Asabe ta ce "ku jira ni a nan zan je na yi aikina,da zarar kun ji yanayin gari ya canza sai ku fito" ta na maganar ne tare da fita cikin akwatin.

Ƴar hudar da ta yi tun daga cikin đaki har izuwa banđaki ta bi,cikin gari ta shiga ta fara jefa tsafinta ta ko ina.Cikin minti da bai wuci biyar ba garin ya fara canzawa ya na yin wani hazo-hazo kamar dusar ƙanƙara na zuba.
Duk mutanen da ba su yi bacci ba a lokacin haka suke fađuwa ba tare da sun san taƙamaimai baccin zai kama su ba.

Mairo ce ta fara fitowa falo inda Tuwalle take kwance ta kalla da idonta,wani haske ta furzar daga cikinsu nan take suka haske baƙar fatar Tuwalle.
Ta yi wani muƙut da yawu hađi da yin kukan mage, Bintoto wacce ke siffar ƙandagaruwa ta rugo da gudu ta na mai cewa "mi ki ka tsaya kallo ga Tuwallen? Hum! Wai ke Mairo ba ki taɓa jin labarin wata marubuciya ba mai suna MRS SADAUKI wacce ta rubuta littafin ABINCIN WANI GUBAR WANI saboda ire-iren ku masu shegen ƙulafuci?"

Daga inda Mairo take ta saka ƙafarta đaya ta mage ta danne kan Bintoto ta na mai cewa "ai wlh ko RUHIN ALJAN ne ke tare da Tuwalle sai na cinye ta"

"Hahaha! To sannu sarauniya NATA MATAR ALJAN ,ai zan ga da wane ƙarfin tsafin za ki cinye ta"
"Zan nemo shi a can ƁOYAYYAR DUNIYA"Mairo ta bata amsa.
"Kar dai ki manta Asabe BOKANYA ce za ta iya yin komi saboda Tuwal...."

Maganarta ce ta yanke sakamakon Inna Asabe da ta shigo,idonta na MACIJI sai wani koren

haske suke fitarwa alamun an yi mugunta sosai.
"Mi ya tsayar da ku ne wai? Ku yi sauri ku fita don ga ƴan uwanku Mayu can tuni sun fara leƙowa kamar uwanda suka san da shirin ku"

Ba su ɓata lokaci ba suka fita,direct gidan Mai Gari suka nufa.
Ba su wani sha wuya ba don dama ba ta ƙofa za su bi ba.
Rashin sa'ar Mai Gari shi ne da ya kwanta bakin ƙofar ɗaki,kamar wasu aikaki haka suka fara kiciniyar fitar da kurwarsa daga cikin gangar jikinsa.
Sun yi nasarar fito da ita amma a wahalce saboda Mai Garin ma ba zaune yake ba,ya na da bokayansa.

Tamkar wata sallah haka Mayun ƙauyen ke ƙetara katangu su na kame kurwar ƙananan yara.Mutanen da ke zube kan titi kuwa sai Hamdullah.

Washegari
Bayan na tashi daga nanauyan bacci na yi miƙa.Wuyana kuwa tuni ya ƙage,fitsarin da ya cika mini mara na fara tafiya na fitsare a kewaye sannan na fito tsakar gida na wanke jikina babu sallah balle salati.

"Inna? Inna?" Na fara kiran sunanta shiru babu amsa, wannan ya saka na shiga ƙurya ɗaki.Tasss abin da ya faru da ni daren jiya ya dawo mini a kai,kusa da akwatin na ƙarasa na a tsorace na buɗe shi sai dai wayam babu komi.
Na ja wata ajiyar zuciya ina cewa "duk ta ƙare Inna ta canza ma Macijinta ma'ajiya,to mage da ƙadangaren fa?" Na tambayi kaina ina tunani can kuma na baiwa kaina amsa "ƙila ƙadangaren ya shige akwati ita kuma mage na jin yunwa ta biyo sa,haka nan ma ne!"

Ihun da na ji a ya karaɗe ƙauyenmu ya saka ni fitowa da gudu ina leƙawa,mutane na gani su na gudu izuwa hanyar da za ta kai ka gidan Mai Gari .
Ni ma na bi bayansu ina cewa "wlh ba a bani labari"

Cirko-cirko mu ka yi a ƙofar gidan Mai Gari,bokaye ne wasu ƴan ƙauyenmu ne wasu kuma na ƙauyukan maƙwabta.
Ɗaya daga cikinsu ne ya fara bayani,da wannan abun mai ƙara sauti "duk wanda ya san shi maye ne mu na son ganinsa a ƙofar gidan Mai Gari in ba haka ba jikinsa zai faɗa masu.Dayawan mutanen ƙauyen nan Mayu ne,jiya maitar ku ta motsa duk jama'ar da ku ka kame kurwarsu ba su ishe ku ba shi ne har da ta Mai Gari .To ku sani kurwarsa ta fi ƙarfin ku

doli ku maido ta ,sannan bayan haka za mu shimfiɗa doka mai tsanani"

Wani abu da ya bani mamaki shi ne yadda wasu mutane ke ware kansu ,ciki kuwa har da Salame ita ce kawai zan iya shaida wa ita ma don ta na abokiyar Inna .

A gaban idonmu aka fiddo Mai Gari wanda yake kwance bai cikin hayyacinsa.Ɗaya bayan ɗaya haka suka yi ta ƙetara shi amma Mai Gari bai tashi ba.
Bokan nan ya sake magana ya ce "doli da sauran Mayun da suka ɓuya,a nan ƙauyen wa ku ke zargin maye ne amma bai zo ba"

Daga inda nake tsaye na waro ido a zuci nace 'goggo Mairo!' na fara dudubawa ko zan hangota,sai dai yadda mutane suka yi cunkoso ban ganin tarin Mayun dukkansu.
Ina tsaka da dube-dube mu ka haɗa ido da Salame,gabana ya faɗi ganin ta na nuno ni da yatsanta.....

*Wanda suka shirya yin payment na MACIJIN CIKI za ku iya farawa 500 complete*  WhatsApp number +22795045822
[27/08 à 11:12] MRS SADAUKI 💫: *MACIJIN CIKI..*🪱

```gajren labari```🪱

MRS SADAUKI 💫✍️

SADAUKARWA ga S REZA

FCWA ☀️

*Page 5*

Da sauri na duƙe ta yadda Salame ba za ta ganni ba.Ina duƙu-duƙu zan tsere kawai na ji an sarɓo hannuna,na zabura na miƙe tare da ƙoƙarin ƙwatar kaina sai dai inaaa tuni Asabe ta kai ni tsakiyar fili.
Duk hankalin mutane ya dawo kanmu,tuni na fara zubar da hawa ita kuwa Salame sai faman cewa take "ita ma wannan cikin ayarinmu take doli ta yi ƙetara"
```

Ina kuka ina ƙari aka saka ni doli na ƙetara Mai Gari,duk da na san ni ba mayya ba ce amma banda zaɓi  doli na yi.
Wani irin baƙin ciki ya turniƙe ni hadī da tsanar Salame.Da ace na san za a ƙaƙaba mini sharrin maita da wlh ba zan je ba .Ina komawa gida na tarar da Inna kwance ta na bacci,kan jikinta na faɗa ina mai fashewa da matsanancin kuka.

"Lafiya? Mi aka yi?" Shi ne abin da Inna ta ce lokacin da ta tashi.
Baki na rawar kuka na ce "ba goggo Salame ba ce ta mini sharrin maita yanzu a ƙofar gidan Mai Gari"
Inna ta bugi ƙirji "ke mi? Ke ce mayyar?" Ta fadī haka ne tare da tashi tsaye,sai kuma ta ci gaba da cewa"ina Salamen take? Ko ta na can har yanzu?" Kai na ɗaga mata.

Cikin sauri Inna ta doshi gidan Mai Gari har ƙura ke tashi sama kai kace Giwa ce .
Mutane tuni sun fara watsewa sakamakon Mai Gari da aka mayar cikin gida.Tun daga nesa Salame ta tsinkayi Inna Asabe, wannan ya saka ta saurin ƙaraso wa ta tari gabanta.
"Ya ne kin ji zafi ne don na saka ƴarki ta yi ƙetara? Hhh! Na yi hakan ne don kowa ya san ke ma mayya ce kawai raina masu hankali ki ke da sunan ke bokanya ce.In kuma ƙarya nake sai ki ƙaryata ni ta hanyar fiddo macijin ki ya yi magana" Salame ke faɗar haka ta na wani riƙe ƙugu.
Inna Asabe ta ce "ko ma dai ni mayya ce ban taɓa lashe Ɗan kowa ba,kin ga kau alhamdullah ke kuwa fa mutum nawa ki ka sanƙame ma kurwa?"
Salame ta ce "Asabe sanin kan ki ne ni na fi gaban ki raina mini hankali,shi jinin da ki ke tsotse ma mutane mine ne naki ne?"
"Na je na tsotsa,ai duk muguntata ban kai ki ba tunda ni ba na kisa iyakata na sha jini ta yadda mutum ba zai mutu ba ke kuma fa?"
Kafin ta kai ga bata amsa ne wannan bokan ya iso gare su "ya aka yi ne?"
Salame ta ce "ita ma wannan mayya ce"
Ya juya ya dubi Inna Asabe su na haɗa ido da ita ya ji wani shock ya ja shi,kallon tsaf ya yi ma Inna a badīni ita ɗin mayya ce sai dai a zahiri duk wanda ya san maye zai iya ƙaryata hakan saboda ita ba ta yawo da kambun maitar ta .
"Ina kurwar Mai Gari wacce ki ka ɓoye?" Ita ce tambayar da ya yi ma Asabe , ita kuwa wani murmushi ta yi sannan ta ce "in kai bokan gaskiya ne ka bincika da kan ka sai ka nemo inda na ɓoyeta tunda har ka yarda ni mayyace" cike da gadara ta fadī haka kuma sam babu tsoro a tattare da ita.
Boka ya buɗe baki zai yi magana kenan Inna Asabe ta yi amfani da ƙarfin tsafinta ta liƙe muryarsa sai ga boka ya koma maganar kurame.
Salame ta waro ido saboda ta yi mamaki sosai ashe duk inda ta ajiye Asabe ta wuce nan,da gudu ta bar gun.
Inna Asabe ta dube shi cikin ido ta na cewa "don duk Mayun Ƙauyen nan sun ji tsoron ka shi ne ka ke tunanin ni Asabe haka nake kamar farar kura? Mtsw " ta ja tsuki tare da yin tafiyarta.

Can ɓangaren Mairo da Bintoto kuwa su na can wani ƙauye.
Cikin gidan tururuwa suka ɓoye kurwar Mai Gari sannan suka tsaya gadinta ,su na jiran mutuwar mai Gari.

Daga cikin ramen su na iya jiyo huci na raɗaɗin azabar da yake ji.
"Za ka ci ƙwal ubanka ne tunda ka shigo gonarmu,wato ka shirya korar duk wani maye da ke ƙauyen ka? To za mu gani in daga can lahira za ka aiwatar da nufin naka" Mairo ke faɗa ta na hararen gidan tururuwar.
Bintoto ta ce "yawuna sai tsinkewa suke na matsu ya mutu ,mu sha daɗin mu"
"Hhh! Ni fa saboda ƙarfin tsafinsa ne zai sa na ci naman Mai Gari in ba haka ba miye na ci a jikinsa"
"Ya ne za mu baiwa Salame ko ya ?" Bintoto ta tambaya .
Mairo ta harareta ta ce "tunda har da ita mu ka sha baƙar wahalar ba"
"Mairo mai Gari ya bar motsi,fiddo mana kurwar"

Mairo ta kai bakinta kusa da hudar ramen ta fara karanto wasu launukan tsafi sai ga kurwar Mai Gari ta fito.
A fannin maita ko tsafi,ana iya raba gadon mutum na muguntarsa.Haka su Mairo suka raba na Mai Gari su biyu ko wace ta haɗiye nan take suka ji sun ƙara ƙarfi a duniyar mugaye,bayan sun gama suka dawo ƙauyen su direct gidan Inna Asabe suka nufa.

Ina zaune kan tabarma ina shan fura abokan Innata suka shigo ko wace ido ya yi mata ja kamar an saka barkono.
"Ke ina uwarki?" Goggo Mairo ta tambaye ni,ban bata amsa ba na ci gaba da shan furata don ni idona ma na baƙin cikin ganinta.
Sai goggo Bintoto ta ce "Tuwalle ina Innar ki?"
"Ta fita tun ɗazu" na bata amsa.
"Mu tsaya jiranta har ta dawo,bari na shiga banɗaki na yi fitsari" cewar Bintoto ta na mai ɗaukar buta.

Sam ban ga tawowarta ba kawai dai na ga wata innuwa ta rufe ni,na ɗago kai mu ka haɗa ido da ita wani koren haske ya fito daga idonta ya shiga nawa.
Ban taɓa sanin akwai raɗaɗi da azaba ba a duniya sai yanzu ,sam na kasa yin ihu kuma.Tsawon minti ɗaya kafin ta sake ni,na mirza idona ina mai sake kallonta da sauri na sunkuyar da kai saboda yadda idonta ke da mugun rikitarwa.

Inna ce ta shigo ta na cewa "yaushe ku ka dawo?" Bintoto kar ki cika mini salanga da kashi"
Na ɗaga kai na kalli Inna ina mamakin ta ya aka yi ta san goggo Bintoto na cikin banɗaki.
"Daga ina ki ke?" Mairo ta tambayi Inna .
"Wajen Salame,don iskanci Tuwalle ta saka ta yi ƙetara don sharri"
"Hum! Ina dalilin wannan hali naki,yarinya ƙarama na gama ki da abokan ki? Wlh duk ranar da ta kawo ƙarata wajen ki sai na cire mata wancan shegen bakin nata" Mairo ke faɗa cikin fushi.

Tuni wani tsoro ya kama ni,sai na ga kamar ta karanci abin da ke zuciyata.Don ina da niyyar shaida ma Inna abin da ta yi mini ga idona amma yanzu kam na fasa wanda ban san cewa babban kuskure na aikata ba.

Hirar su suka shiga yi wacce sam ban fahimta har suka yi tafiyarsu.
Mutuwar Mai Gari ta sauka a maricen yau,tsabar murna ya saka Inna taka rawa ta na cewa "shikenan yanzu kowa ya samu inci" sai kuma ta shiga ɗaki ta fito ta na mai miƙa mini wani tandun kwalli "ungo je ki gidan Mairo ki bata wannan"
Tandun kwalli ne a rufe amma ban san ta ya ya aka yi har nake ganin abin da ke ciki ba tare da an buɗa ba.
Na karɓa,duk da ina jin tsoron Mairo haka na samu kaina da zumuɗin zuwa a can ƙasan raina kuwa na sha alwashin sai na bi didiginta na gano in mayya ce ko kuwa.

Ina tafe ina kallon baƙin hayaƙin da ke ta yawo cikin tandun kwalli har na kawo gidan Mairo.Yau dai kam a buɗe yake,ina shiga na ci karo da magenta sai dai wannan ba wacce ta yage ni ba ce.
Cak na tsaya ina tunanin inda na taɓa ganinta,sai na tuna cikin akwati.
Magen na ƙoƙarin shigewa ɗaki na yi caraf da ƙafarta ta baya,duk yadda na ji ta da nauyi bai hana ni janta giiiii na cilla a cikin tsari wanda dabbobi ke sha.

Sarai na san da mage ba ta son ruwa shi yasa na yi hakan.Dariya na fara har da ƙyarƙyatawa ganin yadda magen ke ƙoƙarin fitowa,tsari na ta shigar mata hanci da baki ta na yin kamar za ta mutu.
Can ta samu ta fito,da gudu ta shige ɗaki ruwa na yi mata tsiyaya.

"Shegiya ke ce na gani ki ka firgita ni a ranar nan ,ni ma na rama" na faɗa a fili,daga can cikin

ɗaki na ji muryar Mairo a shaƙe ta na cewa "Tuwalle shigo mana" ba tare da wani tunani ba na shiga.

A zaune na tarar da ita kan kujera daga ita sai ɗaurin ƙirji,kanta babu ɗan kwali duk gashinta ya yi facacaaa da dusa.Sam ban kawo a raina ba ita ce magen sai da ta tsure ni da ido sosai na hangi baƙin kallon nata,sai kuma na hangi ƙatoton bindin mage baƙi ƙirin sai wani juya shi take. A siffar mutum take amma kuma bindi ne da ita,muƙut na haɗiye yawu yayin da cikina ya ɗuru ruwa.
Mairo ta yi wani makirin murmushi ta ce "matso ki bani saƙon"
Jikina na rawa na ƙarasa na miƙa mata,a gabana ta buɗe tandun wannan baƙin hayaƙin ya fita daga ciki ya shige bakinta.
Ido ta lumshe ta na mai cewa " za ki iya tafiya tunda yanzu kin tabbatar ni mayya ce"

Tsoron da ya shige ni ne ya ɗan ragu har na samu damar yi mata tambaya "to amma mi ya hana ki zuwa gidan Mai Gari?"
Ta bani amsa da "abin da ya hana Asabe"
"Ita Inna ai ba mayya ba ce" na faɗa cikin jin haushi.
"In ki je ki yi mata tambayar za ta baki amsa"
Na ɗan harareta sannan na fito.Ina zuwa a gida na yi wa Inna tambayar,kallona kawai ta yi ba ta ce komi ba.

"Kenan da gaske ke mayya ce? Hum! Inna shi yasa ke da su goggo Mairo ku ka ƙi zuwa gidan Mai Gari"
"Tuwalleeee!" Ta daka mini tsawa,maimakon na ji tsoro sai dai akasin shi.
"Inna ki faɗa mini gaskiya,ni ko mayya ce ke ina sonki haka nan "
"Ita Mairon ta saka ki yi mini tambayoyin? Hum! Za mu haɗu ai"
Daga nan ba ta sake cewa komi ba ta ci gaba da aikinta,ni kuwa fushi na yi don ko abincin dare ƙin ci na yi.

Tamkar yadda ake juya majaujawa haka na fara jin cikina na juyawa,da farko na zata ko yunwa ce sai dai yadda cikina yake ƙaba ya na ƙara zama ƙatoto ya saka ni ƙwala ihu.
Inna kamar jira take ta tashi,fitila ta haska mini ba ta kai ga tambayata ba na fara cewa "wayyo cikina Inna zan mutu"
"Innalillahi ! Mi Mairo ta baki ki ka ci?"ita ce tambayar da Inna ta yi mini .
Cikin kuka nace "komi!"
"Kamar ya komi? Ki tuna dai" Inna ta sake faɗa ta na shafar ƙaton cikina.Tsabar azaba ya saka na kasa yin magana sai kuka,Inna ta sungume ni cikin tsohon daren nan mu ka fita zuwa gidan Mairo.

Abun mamaki can mu ka tarar da sauran wato Bintoto da Salame.Inna ta shimfiɗar da ni tsakiyar ɗaki ta na mai cewa "haka za ki yi mini? Na yi miki dare ke kuma ki saka ni rana?

Bintoto har da ke?" A yadda Inna ke yin magana za ka iya jin rauninta.
Mairo ta ƙyalƙyace da dariya ta na cewa "hhhhh! Ai wlh Asabe ban taɓa sanin ba ki da wayo ba sai yau,tunda har ki ka iya ara mini ƙarfin ikon ki."
Inna ta ce "na ji amma don Allah ki saki Tuwallena ko ma mi za ki yi ki tsaya iya ni"
Mairo ta ce "kin fi kowa sani ban taɓa ɗauka ba na saki,kuma wlh ba zan yi kunya biyu ba"
Salame ta ce "Yauwa ƙawata kar ki saketa ai haka ta yi ta gara ni tare da yi mini baƙar azaba ita ga mai ɗiya"
Bintoto kuwa cewa ta yi "a'a kar ku ce haka,kar ku manta Asabe kullum ta na ƙoƙarinta a kan mu"

"Yauwa Bintoto don Allah ki saka baki ta ƙyale Tuwallena"Inna ta faɗa cikin raunin murya.
Ihu na kuma saki ina cewa "Inna shikenan za su kashe ni wayyo cikina zai fashe"
Ban ida rufe bakina ba Inna ta yi wani furuci nan take ta rikiɗe ta zama ƙatoton MACIJI .....

Littafin kuɗi ne katin MTN na 500 za ki biya domin ci gaba complete,wacce ta shirya ta yi mini magana ta WhatsApp +22795045822
[27/08 à 11:13] MRS SADAUKI 💫: *MACIJIN CIKI..*🪱

```gajren labari```🪱

MRS SADAUKI 💫✍️

SADAUKARWA ga S REZA

FCWA ☀️

*Last free page 6*

Zamantowar Inna MACIJI ba shi ya fi ban tsoro ba,a'a yadda ta rinƙa kumbura ta ƙoto ta ƙara zama gibjejiya kamar icce don har sai da ta kusa taɓo rufin ɗakin.
Duk tsoro ya bayyana a fuskokin ƙawayenta,washeshen bakinta ta buɗe ta na mai zuro shi ta ɗauke Salame ta fara taunawa kai kace mai cin abinci.
A gaban idona Inna uwa mahaifiyata ta haɗiye mutum.Cikin tsoro goggo Mairo ta buɗe bakinta ta zaro wani abu sannan ta nufo ni,ta na shafar cikina duk komi ya koma normal sai na ji duk
```

azabar ta tsaya haka kumburin cikina ya sace.

"Haaam ! " Ta yi wata hargowa ta na mai juyowa saitin mu ni da goggo Mairo.Yadda ta ƙara wangale ƙaton bakin macijin nan mai ɗauke da zaƙa-zaƙan haƙora ya saka hantar cikina kaɗawa.Ta sunkuyo kanta yawu na mata zuba,ɗan guntun kallabin Salame ka na iya hango shi laƙe da haurenta.

Gutsur! Ta gindile kan goggo Mairo da haƙoranta,gangar jikin ta faɗi ƙasa yayin da kuma kan ke cikin bakinta.Kaina tuni ya fara juya,kafin wani lokaci numfashina ya yi mini ƙaranci ban sake sanin abin da ya faru ba sai tashi na yi na tsince ni kan shimfiɗata.

Duk abin da ya faru ne ya dawo mini akai,sai dai kash ƙwaƙwalwata ta kasa ɗauka balle har zuciyata ta gamsar da hankalina kawai sai nace mafarki ne nake .
Sai dai ba aje ko ina ba na gaskata lamari.Bayan na dawo daga banɗaki na shiga ƙurya ɗaki da zumar neman Inna ,ban kai ga buɗa baki na kira sunanta ba na yi tuntuɓe da wutsiyar MACIJI gudar ƙatuwa har sai da na yi tangal-tangal zan faɗuwa ƙasa .
Da taimakon bindin na faɗa kan gangar jikinsa,a hankali kuma ya warware bindinsa.
Zuciyata sai faman bugawa take,duk a tunanina macijin Inna ne sai dai ashe abun ya wuce haka.

"Tuwallena ni ce Innar ki,kar ki ji tsorona saboda ke na gwammaci na zama macijiya akan na bari a cutar da ke" muryar Innata ce amma baki da gangar jiki na MACIJI ne da ita.
Ta na maganar ne ta na wani shafar fuskata da bindi,ban san mi yasa na ji duk tsorona ya gushe ba.Ƙila sanin ita ɗin garkuwata ce ba za ta bari wani ya cutar da ni ba balle kuma ita ta yi wannan gangancin duk da zamantowar ta macijiya.

Na rungumeta ina kuka na ce "Inna don mi yasa ki ka zama mayya? Mi ya sa? "
"Ba son raina ba ne Tuwalle,ni ma gada na yi gun mahaiyata.Je ki yi mana girki na fara jin yunwa"
Na ɗan ɗagata ina kallon idonta da ba su da kyawun gani,na ce "Inna shikenan yanzu ba za ki sake komawa mutum ba?"
"Zan koma sai lokaci ya ya yi" ta bani amsa.
"Yaushe kenan?" Na sake tambayarta.
"Sai in kin girma sosai a lokacin zan rikiɗe na dawo mutum saboda ƙarfin ikon ki"
Ba tare da na fahimci mi take nufi ba na tashi na fito waje na ɗora mana ɗumame.

Bayan na gama na zuba shi a cikin kwano na shiga ƙurya ɗaki.Da hannuna na rinƙa baiwa Inna macijiya abinci a baki har ta ƙoshi.
Mu na nan zaune sai ga Bintoto,ba tare da wata doguwar hira ba ta ce "Asabe ya kamata mu bar ƙauyen nan kafin a yi mana tonon silili,tuni an ɗora sabon Mai Gari kuma tsanani ne da shi"
Na kalli goggo Bintoto a zuci nace 'oh ! Ita Inna ba ta haɗiye ta ba kenan?'
"Ni ma na yi tunanin haka amma kin san ba zan tafi a haka ina macijiya ba,doli sai an samu wajen da za a ɓoye ni "Inna ta faɗa ta na wani kaɗa taɓaɓen kanta.

Goggo Bintoto ta fiddo wani ɗan kwagiri irin wanda tsofi ke ɗaurawa a ƙugu don zuba kuɗi,sai dai wannan shi azargagi ne da shi.
"Ga inda za ki shiga nan" ta nuna mata,Inna ta ce "to babu matsala gobe sai mu tafi, yau za mu haɗa duk komi namu"

"To gwara ku fara tun yanzu don garin hadari ne da shi" cewar goggo Bintoto ta na mai yin tafiyarta.
Bayan fitar ta ne Inna ta faɗa mini abubuwan da za mu tafi da su,ni kuwa duk na haɗe su wuri guda.

Ruwan sama suka fara zuba kamar ga bakin ƙwarya an ɗauki dogon lokaci bisanin a tsagaita.
Kamar mai jira haka na fito tsakar gida tare da nufar hanyar da za ta kai ni ƙofar gida.
Wani kuka ne ya ja hankalina,na fara waige-waige har idona ya sauka wurin da na taɓa ganin Inna duƙe ta na rufe wani abu.

Daga nesa a inda nake tsaye ina iya hango yadda can ƙarƙashin ƙasa yadda wani abu ke ta bada kalolin wuta sai haske yake.
Ƙafafuwana har ƙaiƙayi suke wajen saurin isa,na duƙa tare da sa hannu na fara tonon ƙasa wacce ta jiƙa ta yi taushi.Ina tono har na isa ga wani ɓawan ƙwai fari sol wanda ya ɗan yi huda ƙadan.
Ko kafin na ida cirosa wani ɗan jaririn MACIJI ya fara fito da kansa,ba tare da jin tsoro ba na yi masa tarba mai kyau kan tafin hannuna.

Ɗan mitsitsi ne sosai,jikinsa kori da baƙi ne .A hankali nake ware idona ina sake kallon shi,na shagala sosai sam ban farga ba har ya huda jijiyayar hannuna.
A gaban idona macijin nan yake kurɗa jijiyar hannuna har ya shige duka,ruf hudar da ya shiga ta rufe sai dai a saman fatata ina iya hango ƙyallinsa ,ina kuma jin yadda yake tafiya cikin jikina.

Wani abu na fara jin ya na mamaye ni kamar wacce ta sha ƙwaya,idona kuwa har wani yaji na ji

su na yi.Kafin wani lokaci hannuna ɗaya ya rine ya yi baƙi hadɗi da ɗaraba-ɗaraba kamar jikin MACIJI .

Duk mai son complete sai ta biya 500  katin MTN ko transfer,wacce ta shirya sai ta yi mini magana ta WhatsApp +22795045822